Zuwa yanzu gaba aya falon babu wanda rauni bai rufesaba.

Mamy kam itama tuni hawaye takeyi.

Dr Sajo ma kife kansa yayi, bisa hannun kujerar yana zubda hawaye.

Alhaji Bala Tambari, kuwa rumtse idanunshi kawai yayi yana mai jin rauni.
Riyyam-nsra da Ramadan kuwa, idanu suka zubawa Barrister.

Shi kuwa Barrister cikin Muryar kuka yace.
arainiyace, maraici mafi muni, marsicine da ban ta a jin irinsa ba a duniya koda a littatafai da finafinai.
Domin maraicine da ita kanta bata saniba maraicine da aka hana ta amfani iyayenta bayan ransu, maraicine da ba'a bata ofar yiwa iyayenta addu'a ba, sabida masifar son duniya. Yah Idi da hannunsa ya kashe an uwanmu aninsa mai binsa ni kuma yayana da nakeki.

Zuwa yanzu wani irin tsuma jikin Jannart ya farayi tare da jin wani irin tashin hankali yana ziyartota.

Shi kuwa Barrister Kabeer cikin rauni yaci gaba da basu lbrin kamar haka.
u uku kacal iyayenmu suka haifa, Yan Idi shine, Babba sai Yah Abdulkareem, kana nine karami.
Iyayenmu sun renemu cikin aminci da bamu Kekkyawar tarbiyya.
Har muka girma, Yah Idi ya fa a kasuwanci, cike da zalamar ganin ya zama shahararren mai ku i, shi kuwa Yah Abdulkareem ya bawa karatu mahimmanci, inda burinsa ne ya zama cikekken lawyer.
Allah kuwa ya cika masa burinsu.
To amman fa Yan Idi baya godewa Allah kan abinda ya basa, shiyasa kullum na wani yake hango, ya samu abokai masu irin zuciyarsa.
Haka yasa mugayen zu atansu ha ewa.

Yah Idi yayi aure, matarsa Amina mahaifiyar Junaid kenan.
Kana bayan ita, ya auri Momynsu Azeez amman ita a ar sokotoce kuma acan ya ajiyeta, shiyasa.
Basu wani san junaba.
Amina tunda ta aifi Junaid bata ara haihuwaba sai bayan shekaru goma, Allah ya bata ciki.

Momynsu Azeez kuwa ta Haifi Azeez wanda shekara uku ya bawa Abdul.

A lokacin kuma Yah Abdulkareem ma yayi auren, da ya kasance ba zata, domin aurene da akayi komi, da komai cikin □an □anin lokacin.
Ya auri Aunty Zee, daga ranar kuwa.
Yacewa, iyayenmu zai □aukeni.
Zan dawo gidansa da zama.
Haka kuwa akayi basu hanaba.
A lokacin in secondary School.

A watan da akayi auren a watan Allah yayiwa iyayenmu rasu baki □aya su.
Dama ba yawan dangine da muba.
Yah Abdulkareem mutum ne mai jin □ai da tausayi da gsky.
Aunty Zee kuwa wata daya da aurenta ta fara laulayim cikin.
Wanda sam bata son taji duk wani abu na □amshin girki.
Toh dan lokacin mafi akasarin lokuta nikeyi mana girki.
Aunty Zee macece mai ha□uri da sanyin hankali.

A haka taita rainon cikinta har ya cika watannin haihuwarsa.

Wata rana da yamma Yah Idi yazo.
A falon Yah Abdulkareem din suka zauna.
Ni kuwa ina falon Aunty Zee muna kallo, sai take cemin, inje in amshi ku □i in seyo mata, kifi, don lokacin cikin ya kai haihuwa Yau ko gobe amman bata iya cin komai sai kifi.

Da sauri na mi□e, na nufi □ofar falon Yah Abdulkareem din.
Har nasa □afa zan shiga sai kuma na tsaya sabida jiyo muryar ya idi da abinda yake fa□a.
Abdulkareem ka bamu goyon baya, a kan wannan □udurin namu, domin shine ka□ai kwanciyar hankali ka, sabida shi kansa uban gidan naka, yace mana takardun suna hannunka ya baka ka dawo dasu, a soke aikin, dan haka ka bani su, tun muna shaida juna.
Shi kuwa Yah Abdulkareem sai naji yana mgnar cikin sanyi yace.
□□mman ai cewa yayi kawai a tsaida aikine bawai in baku, takardunba, ya za'ayi in baku abinda ba nawaba Kuma ba nakuba, inci amanarsa kenan.

Gyara tsayuwata nayi a bakin □ofar jin Yah Idi na cewa.
Wallahi ina garga □inka Abdulkareem domin, shakka babu, zan iya yin komai a kanka, ba tare da duba ala□armu ba, muddin zaka hanani cika burina.
Da sauri naja da baya jin Yah Abdulkareem na cewa.
□□asan zaka aikata, kuma nasan duk abinda zakayi bazai wuce, ka kasheni ba, to wlh koda kasheni zakayi bazan bada suba.
Hakan da yace ya fusata Yah Idi sai ji nayi yace.
Zaka ko gani ganin idonka.
Sai nayi saurin barin wurin sabida jin yana fitowa.

Saida ya tafi, na shiga na samu Yah Abdulkareem yayi shiru, cikin sanyi nace masa Meta faru,? Bai □oye min komaiba, kana ya □ara da cewa.
Nasan son zuciya da rashin tsoron Allah irin na Yah Idi wlh zai iya min komai fa Kabeeru.
Naji tsoro sosai.

Dan haka, zan baka takardun nan, ka ajeyimen su.
Dan Kada in ya turo su sani in basu.
Cikin yarda dani yamin wannan bayani.
Kana ya bani takardun.

Sannan na gaya mishi mishi aiken da akayi min.
Ya bani ku□i naje, na saya mata.

Muka dawo muka zauna a falon munata hira, tanacin kitinta.
Saida ta gama sannan na tattare Wurin Yah Abdulkareem na dariya wai ta medani kande.
Ita kuwa sai ta zuba mishi ido tare da cewa.
Shekaran jiya da zaka tafi Gembu naso in bika, muje, amman nasan hanyar gashi kuma yadda nake, sai nakeji dama na gaya munje nayi musu kallon karshe.
Da sauri yace mata.
Zainab kallon □arshe kuma?
Sai tayi murmushi tare da sunkuyar da kai, mu kuwa duk ido muka zuba mata, cikin sanyi tace.
Musamman Neena na, naso in ganta ta ganni. Amman ba komai Allah ya sadamu a darussalam.
Wannan kalma ta girgiza Yah Abdulkareem dan a take naga yana zubda hawaye.
Ita kuwa da sauri ta yun□ura zata tashi.
Sai kuma ta koma ta zauna tare da ri□e cikinta.
Wachhh Abban Jannart yau kam da alamun Jannart zata fito duniya.
Jin haka kuma ya samu murmushi domin haka take tanada, raha, shiyasa tun kafin ta haihu take cewa, in dai ya mace ta haihu Jannart za'a sa mata in kuwa na mijine Jalaladdeen. Haka yasa take kiran Yah Abdulkareem da Abban Jannart tana yawan cemin idan mace ta haifa dai to matar Rayyern ce, wai sabida tana son yaron ni kuwa a lokacin banma san waye Rayyern dinba.
Shi kuwa Yah Abdulkareem murmushi yayi tare da cewa.
Wai da gaskene Zainab? Kai ta jinjina masa tana matsa la □□anta kana zufa na tsastsafo mata tace.
Allah kuwa da gaskene.
Da sauri nace, bazaki jira in zama likita ba, in kar□i haihuwar da kaina. Dan a lokacin dani da Yah Abdulkareem duk burinmu in karanci likita, ita kuwa Zainba da sauri ta kamo hannun Yah Abdulkareem.
Ganin haka yasa muka tafi asibin Dr Lukman, duk da Dr Sajo abokinsa ne, to amman lokacin baya□asar.
Muna zuwa kuwa aka amsheta, ana dubawa ma, akace ai yanzun zata haihu.
Muko sabbin shiga dama bamuzo da kayan haihuwa ba, hakan yasa, nayi maza nace zan koma gida in□auko.

Ina fita kuwa, tana haihuwa.
Dr Lukman kuwa da kansa ya amshi haihuwar sabida, a lokacin babu yawan likitoci mata.

Cikin□ankanin lokacin na dawo, ina dawowa, na samu.
Yah Abdulkareem a ki□imi, yana bin Dr Lukman yana masa Dr Lukman, ka taimaka asan abin yi, jinifa ya□alle mata.
Shi kuwa Dr Lukman waya yakeyi, haka yasa sai hannu yake juya mishi alamun yana zuwa.

Ni kuwa sauri nayi na shiga, cikin□akin da naga sun fito.
A kwance na sameta da alamun har an gyara baby, da sauri ta yafitoni da hannu, ina isa, tasa hannunta ta□auko Jaririyar daga kwance cikin jan numfashin tace.
Kabeeru, ga Jannart ta samu, amman zata rayu marainiya, babu uwa, kuma ubanma babu tabbas, domin naji abinda Dr Lukman yake fa□awa Yah Idi a waya kafin ya fita, a zatonsa bana jin turanci tunda ni ba fulatar Gembu ce.
Jini nake zubarwa amman cewa takeyi bazai min allurar tsaida jininba, bazai kuma gayawa Abban Jannart ba sai yaga na kusan mutuwa, yace kuma yanzu zaiyi □o□

arin tura musu Abbab Jannart ya tafi gida, suje can su sameshi, wai in har bai basu takardun ba su kashesa kamar yadda sukasa aka kashe Alhaji Bashir Maigaskiya daren jiya,
Cikin tashin hankali nace. Yah Idi Kuma, to shi yana ina, cikin jan numfashin tacemin shima yana cikin asibitin nan ya kawo Aunty Amina itama haihuwa zatayi, kuma naji suna cewa, ta rasu, abinda ta haifama babu rai.
Kabeeru, nasan ni kam bazan rayuba, kuma inaji a jikina zasu kashe Abban Jannart, dan Allah ka zame mata Garkuwa bongo abin jingina, ka ji □anta, ka bata dukkan kulawa, da Kekkyawar tarbiyya, in ta girma kayi mata zabi da miji na gari mumuni mai jin tausayin maraicinta, Dan Allah Kabeeru kada ka bari, rayuwarta ta taggayara ko ta wula □anta, ina tsoron kada magautan mahaifinta su dawo kanta.
Dan girman Allah Kabeeru kayi min al □awarin kare min ita daga dukkan abin cutarwa, ka gaya mata ina sonta mahaifinta na sonta, tun kafin zuwanta duniya, ita kuma ta somu bayan barinmu duniya, tayi mana addu'a, ta zame mana al'waladussaliha.
Hankalina bai tashiba sai lokacin da na amshi yarinyar daga hannunta domin da ka gani kasan □iyarta ce.
Sai kuma □an □aramin yatsarta na hannun hagu da farcensa yake kamar a tsage kuma kala biyu, wanda irin farcen yatsar Yah Abdulkareem ne sak da sak.
Sai kuma na sunkuyo zan kalli fuskar Aunty Zee.
Nayi masifar gigitaccewa lokacin da naga idanunta na kafewa sunayin sama numfashin ta nayi □asa.
Cikin tsananin tashin hankali na kwantar da yarinyar, tare da tallabo kanta ina cewa.
La ha ila ha illahu Muhammadu Rasulullahi sallahu alaihi Wasallama.
Nayi kamar shadarne sabida firgicin ganin kamar ranta na barin jikinta ne, ita kuwa cikin sassayan murya ta amshi kalmar shahadar tana nanatawa, kira na fara aunawa Yah Abdulkareem lokacin da takai karshen kalmar shahada na ukun da kuma fitan ranta.

Ya salam naga tashin hankali a wannan ranar.
Domin a ki□imi na fito, sai dai ina fita motar Yah Abdulkareem na barin wurin.
Ban san me Dr Lukman ya gaya mishi ba yasashi komawa gida.
Babur na hau a guje nabi bayansa.

Sai dai ya rigani shiga gidan,

Cikin ki□ima nabi, bayansa, bayan na sallami mai babu □in.
To sai dai bai tafiba ganin yadda nake kuka sai ya tsaya yana kallona.
Koda na shiga sai ya biyoni sabida bani canjina.

Ni kuwa da sauri na nufi falon jin wani irin masifeffen ihu mai ha□e da salatin da Yah Abdulkareem yakeyi.
Ina isa bakin □ofar na hango Yah Idi ne ri□e da wu□a, yanata caccaka cikin Yah Abdulkareem dashi. Alhaji Abdu Tababa na gefensa yana she□a dariya.
Ihu nasa da azaban □arfi zan shiga, cikin.
Cikin zafin nama mai Babur nan ya fincikoni tare da fara jawoni waje.

Su kuwa a cikin inaga ihun da salatin da Yah Abdulkareem yakeyi ne ya hanasu jiyo nawa ihun.

Shi kuwa mai Babur nan da yake babbane da □arfi ya jani ya hau kashin sani.
Bayan layinmu ya tsaya jikin wani kango.
Yana cewa.
Kada kaje zasu kasheka dan Allah kada ka shiga, zasu kasheka yadda suka kashe na cikin.

Ni dai daga nan ban kuma sanin ina nakeba na suma.

Lokacin dana farka kuwa Yah Idi na samu a kaina.
Ashe shi mai Babur din da yaga na suma asibitin □aya daukoni ya maidani, yayi komai aka bani gado sai ya gudu, sabida yana tsoro.
Toh da Dr Lukman yaga nine sai ya sanarwar Yah Idi.
Ashe kwanana uku ban dawo hayyacina ba sai ranan.
Ina farka sai na bushe kawai ina kallon Yah Idi sabida yadda ya ruggume ni yana wani irin masifeffen kuka mai tada hankali yana cemin. Wayyo Kabeeru mun rasa Abdulkareem sabida rasuwar matarsa Zainab da □ar data haifa, shima zuciyarsa ta buga ya rasu, sannan Amina ma ta rasu, sai wurin haihuwa sai marainiyar □arta data bar mana, Kabir ina tsoron rasaka, in ka rasu bani da kowa nawa a duniya.
Tsoro mai tsanani ne da mamakin makircin Yah Idi ya rufeni ya hanani Koda motsi.
Wanda da haka ya yaudari mutane haka yasa ko jami'an tsaroma basu shiga mgnar ba.

A ranan aka sallameni dole gidansa muka koma, inda muna zuwa na samu ya □auko Mammynsu Abdul daga Sokoto ta dawo da zama nan gidan sa, ya kuma dam□a mata Jannart a hannunta, da cewar □ar da Amina ta haifane.

Tsoro da fargaba ne yasa dole na kasa yin komai gashi bani da wani hujja bare shaida ga yarinta.
Sai dai nasan tabbas □an sa Aunty Amina ta haifa ya rasu dansu □a na mijine ba, kamar yadda Aunty Zee ta gaya min,
Sannan na gane Jannart, duk kuma wanda yazo sai aita mamaki ana cewa.
Wannan kam kamar □ar Zainab, to wannan abinne yasani yin shiru domin nasan bani da □arfin da zanyin fa□a fito na fito dashi.
Haka yasa na shiga jikinsa na zauna a gidan ina kula da komai na Jannart da rainonta Junaid kuwa yana sonta sosai.
Sai dai tana girma daga shekarunta goma sha hu□u abin ya fara sauyawa.

Sai ya fara sha'awarta, ni kuwa a lokacin nayi aure babu yadda banyiba, Yah Idi ya bani ita amman sai ya□i fir dole na ha□ura Amman babu randa gari zai waye ban jeba.
Sai daga baya na fahimci ita kanta Jannart ya fara sha'awar kasheta sabida yaga sa hannunta irin na mahaifinta ne sak.
Toh sai yake rainonta dan ta cika shekara ashirun da biyu, tasa mishi hannu a dukkan takardun kadarorin mahaifinta, a matsayin ya mallaka masa su kafinma ya rasu, shiyasa ya rainentan kuma yake da gudurin kasheta.
Wannan dalilin ne yasa, na fara shirin neman inda zan boyeta.

Kwatsam ranar a wurin taron mu sai naga Rayyern, kamanninsa yasani tuno da Alhaji Bashir Maigaskiya, ashema mahaifinsa ne, ina kallonsa a lokacin tamkar wanda aka haifa dan □aukar fansane.
Daga nan nayi ta bibiyar rayuwarsa, na kuma gane shi asalin □an Alhaji Bashir Maigaskiya ne, saidai bani da hujja, da naga Baba Mau□o kuwa naso in gane da tafiyarsa.
To amman bai bada damaba.

Wannan mai Babur □in kuwa yanzu haka yana cikin tawagar Yan Idi, shi Al□ali Baba,
Muna tsara komai tare, da hakane muka samu cikakkun hujjojin da Yah Idi ya rin□a fa□a mana dukkan abinda yayi. Yayinda kuma muke na□an hakan a video komai.
Sannan Al□ali Baba babban al□aline da akeji dashi.
Kama kuma ga Alhaji Bala Tambari shima duk tawagar mu□aya.

Zuwa yanzu duk munada cikekkun hujjoji na musamman.

Da sauri duk falon suka juyo kan Jannart, da ta saki wani irin maraitaccen kuka mai cike da maraici da □unan rashin iyaye.
Fa□awa jikin Rayyern tayi tare da kife kanta bisa cinyarsa.
Wani irin masifeffen kuka mai tafiya da numfarfashi ta sake cikin shesshe □an raunataccen kukan take cewa.
□□nnalillahi wa innailaihi raji'un, Hasbunallahiwani'imanwakil, wayyooooooooo Allah na, niyi asarar rayuwata ta, tsowon shekaru ban amfani iyayena da komaiba, kuma wai ina raye, banyi musu amfani ba ko ka□an ban zame musu mai tunasu da addu'a ba, wayyooooooooo Naaaan zuciyata zata fashe,□□.
Ya Salam shima kansa Rayyern fashewa yayi da □a □□arfan kuka mai sauti, ya jawota jikinsa ya ruggumeta da karfi.

Barrister Kabeer ma kukan ya saki kamar zai shi□e,
Baba Mau□o ma kife kansa yayi bisa sawun Alhaji Bala Tambari dake gefensa yasani kuka mai rauni.
Aunty Dijat kuwa itama ruggume yaranta tayi tare da sakin kuka.

Abba kuwa shima kukan yakeyi yana □an bubbuga kafa□ar Barrister Kabeer alamun yayi ha□uri.

Riyyam-nsra, Ramadan, Mammy da Mamy kuwa tausayin Jannart ne yasasu kuka mai ciwo.

Shi kuwa Rayyern cikin kuka yace.
□□ooo! Nooo!! A'a Janna bakiyi asarar rayuwaba kuma suma basu yi asarar haihuwar ki ba.
Tsinenne kuma la'annne Alhaji Idi Sale Dakata shine yayi asarar rayuwar duniya data □iyama.
Daya tauye miki maraicinki
Yabar azzalumi □ansa yana cutar min da ke.
Baki da laifi domin a baibai ya barki kika rayu.□□

Cikin kuka mai tafiya da numfarfashi ta kara ruggume shi tare da cewa.
□□aaan kaji fa Mamana ta bada ya□ini akan zan rayu, har tana cewa acemin suna sona tun kafin zuwana duniya.
Sannan tana bada wasiyan a sanarmin in sosu bayan barinsu duniya in rin□a tunasu da addu'a.
Amman aka hanani wannan damar, Naan dame na amfanesu, me ribar haihuwata da sukayi? in banda cikin watannin nan daka nusar dani dayi musu addu'a a cikin dukkanin sallolina□□.

By
GARKUWAR MARUBUTA
1/2/22, 16:17 - Auntyn: Ya salam kusan gaba□aya falon□ibkewa da kuka sukayi.
Shi kuwa Rayyern kukan yakeyi har yana jin kamar kanshi zai buga, cikin tsananin tashin hankali ya tallabo kanta ganin yadda take kuka tuni idanunta sun kumbura sunyi jazir.
Hancinta yayi ja, numfashin ta sai korar juna yakeyi, hakan ne yasa ya jawota jikinsa ya ruggumeta da samun dai-dai ton numfashin ta.

Cikin tsananin tashin hankali Baba Mau□o ya fara maimaita.
□□nnalillahi wa innailaihi raji'un Hasbunallahiwani'imanwakil□□.
Hakan yasa suma kan suka fara maimaita hakan.
Wanda a take Allah ya fara sau□o musu da sassauci cikin zu□atansu.

Sai kuma duk suka fara sau□e ajiyan zuciya amman banda Jannart da har yanzu maimaita innalillahi wa innailaihi raji'un takeyi tana kuma mai ci gaba da kuka.
Cikin sau□e ajiyan zuciya Barrister Kabeer yace.
□□i gafarceni Jannart ki dena kuka, na yi iya iyawata dan ganin komai ya tafi dai-dai.□□
Shi kuwa Rayyern cikin sanyi yace.
□□arrister batar tayi kuka! Idan batayi kukaba a yau sai yaushe zatayi kuka, inama ace labarinki yazo kamar namu Janna ace iyayenki na raye, amman kash haka bata kasance ba.
Kiyi kukan rashinsu da kuma □oye miki da akayi, amman kada kiyi kukan maraici.
Nayi miki al'□awari zan cike miki dukkan gurbinsu.
Zan sama miki farin ciki.
Mammyn na zata zama madadin Mamanki Baba Mau□o zai zama Madadin babanki.
Kisa a ranki Zaiton da Riyyam-nsra sune □anneki.
Ga Hafeez da Hafiza ga Abba Kabir □inki.□□

Shiru Abba da Barrister Kabeer sukayi suna mai kallonsu da sauraron kalamansa.

Baba Mau□o kuwa da Mammy kai suka jinjina mata alamun eh hakane.
Ramadan da Riyyam-nsra ba cikin tsananin tausayinta sukace.
□□y Aunty kiyi ha□uri, ki dena kuka in Sha Allah bazamu sake barin kiyi kukaba□□.

Shesshe□an kukan ta fara ja da□arfi.
Sai dai ina abin yaci tura.
Haka yasa Rayyarn kuma ruggume ta, Allah ya sani ya mance ma a cikin mutane suke, yana kuka yace.
□□anna ki kalleni in Sha Allah zan zame miki Nagartaccen miji mai jin□ai, tausayi, kulawa, sadakarwa, zan zame miki bongo abin jingina, kuma garkuwa ga duk wata cutarwa da izinin Allah.□□
Kai kawai ta fara gya□a masa yana kwato numfashin ta, amman ina, cak numfashin ya tsaya ta lafe jikinsa a sume.

Cikin tashin hankali ya□an janye jikinsa, tare da jera mata kira.

Ramadan ne ya mi□a da sauri yana cewa.
□□a salam Hamma Rayyern suma tayi fa□□.
Gaba□aya hankainsu ya tashi, hakan ne yasa duk sukayi kanta.
Mammy ce tasa hannu ta amsheta daga jikinsa sabida ganin yadda gaba □aya jikinsa yake karkarwa, ya kasayin komai.
Aunty Dijat ce ta mi□a da sauri ruwa ta kuma□auki wa mai sanyi.
Tana mi□a musu, cikin sauri Mamy ta yayyafa mata a fuska an kuwa yi Sa'a ta farfa□o da wani sabon kuka.
Ruggume ta Mammy tayi tana mai □an shafa bayanta da tausar zuciyarta da sanyaya kalamai.

Jin kiran sallan mangarib da akayi ne yasa, kab mazan sau□e numfarfashi tare da mi□ewa, suka firfita haraban gidan al'wala sukayi kana kab suka nufi masallaci.

Matan kuwa, cikin sanyi Mammy ta mi □a tare da kamo hannun Jannart daketa shesshe □a ta mi □ar da ita.
Mamy ce ta nuna mata □akin.
Sai kuma Aunty Dijat da Zaiton subabi bayanta.
Cikin sanyi da lallashi Mammy ta kalleta lokacin da suka shiga cikin □akin cikin tausasawa tace.
□□annart kiyi ha □uri kinji ki dena kuka, ki shiga bathroom ki watsa ruwan sanyi, zakiji sanyi a zuciyarka.
Sannan kiyi al'wala kizo kiyi salla, a karo na forko a rayuwarki, ki □aga hannunki, kiyiwa iyayenki addu'a shine abinda mahaifiyarki ta ro □a, kuma shine zai sasu farin ciki ba kukanki ba.
Kana kiyi sujjada ki godewa Allah da ya hana magautanka samun nasara a kanki ya rayaki har kika san gsky□□.
Cikin sanyi ta gya □a mata kai.
Ganin haka yasa ta tallabeta suka shiga bathroom din.
Kana ta fito tare da ja mata □ofar.

Su kuwa su Aunty Dijat da Zaiton main falon suka koma, a bathroom □in ciki sukayi al'wala, kana Mammy ma nan ta fito, al'walan.
Mamy kuwa sallayu ta shisshin fi □a musu, kana duk suka kabbarta sallah.

Acan masallacin cikin gidan kuwa suna idar da salla, Baba Mau □o yayi ta jerowa su Barrister Abdulkareem addu'o'in neman musu gafara da samun ni'imantaccen makwanci.

Ana shafawa Rayyern ya sulale ya fito ya nufi cikin gida.

Ido ya □an zuba musu ganin duk suna cikin falon, ganin bai ganta bane yasashi.
Wuce □akinta.
Jiyo shesshe □an kukanta a bathroom ne yasashi kutsa kai ciki.

Cikin bathtub dake cike da ruwa ya hangota tana zaune cikin sa babu komai a jikinta sai, kuka takeyi har jikinta na rawa.
Da sauri ya iso inda take, ita kuwa jin motsin mutum ne yasata □ago kanta, ganin shine yasata, yin saurin matsowa bakin bathtub □in, hannunta tasa ta ri □e sawunsa tana daga ciki.
Kanta ta manna kan sawunsa, cikin tsananin rauni da kuka tace.
□□aan Zuciyata, ta □untata, ruhina ya girgiza a sanadin rashin muradin zuciyata Naan bani da kowa duniya□□.
Da sauri ya zauna bakin bathtub □in kanta ya manna da cinyarsa cikin sanyi yace.
□□ina dani Jannart, ki dena cewa haka, kina dami, kuma zamu samar da zuriya maiga □i, zanyi miki ciki ki haifa mana yara da yawa, gani ga yaranmu ga Mammy ga Mamy ga Abba ga Baba Mau □o gasu Abba Kabeer ga Zaiton kinaji Aunty Dijat da Mamy har sunayi mana kallon mai ciki, da ace haka zai tabbata da nayi farin ciki □□.
Cikin sanyi ta fara sau □e ajiyan zuciya jin yadda yake □an watsa mata ruwan sanyin a jikinta.
Ganin tayi shirune, yasa ya tasheta, ya zubda ruwan bathrobe ya zira mata, kana yasa tayi al'wala kana suka fito.
Shi ya taimaka mata ta, shirya kana yasa mata hijjabi.
Ta kabbarta sallah.
Shi kuwa falon ya fito.
Nan ya samu su Mammy na zaune, da alamun jira sukeyi isha tayi suyi salla kafin su tashi.

Shi juyowa yayi ya kalli Ramadan daya le□o tare da cewa.
□□amma Rayyern Abba yace kazo, muyi salla isha ta □arato □□.
To yace kana yabi bayansa, so yake yayi sallan ya rabu da kowa yazo ya kula da Jannansa.

Bayan an idar da salla ne.
Mamy ta kai musu abinci falon Jannart.
Kana Mammy kuwa ta shiga ta fito da ita.

Su Abba kuwa a babban falon suka shigo baki □ayansu, a nan inda Mamy da Zaiton suka jera musu abinci suka zauna.

Gaba □ayansu babu wanda ya ci wani abincin kirki.
Ita kam ma Jannart kuka ta sawa Mammy data matsa mata taci, abinci sai Mamy ce ta tsoyayo kunu tare da mi□awa Mammy tace.
□□i inaga gaba □aya ma cikin yanata cin abinci, dan tunda suka dawo in Banda kunu batasha sa wani abu a bakintaba sai □azune ma ta □anci a logoi alogoi.□□
Cike da tsananin tarin farin ciki Mammy tace.
□□asha Allah! Masha Allah!! Masha Allah!!! Alhamdulillah! Allah ya in □anta ya rabaku lfy□□.
Sunkuyar da kai tayi tana mai tsiyayar da hawaye, ita kuwa Mammy mi□a mata cup □in tayi.
Amsa tayi tana mai zubda hawaye, sun sa mata son haihuwa musamman yadda Naan yake nuna mata in cikine zaiyi farin ciki da yadda ya nuna mata da haihuwa ne kawai zasu fa□a□a ahlinsu.
A hankali ta kurbi kunun sabida yadda Aunty Dijat ke ha□ata da Allah tasha kur□a takeyi hawayen na zubar mata.

Su kuma haka suka □an tsastsakali abincin sama-sama.

Acan falo ma haka mazanma basu wani ci abincin kirkiba.

Rayyern ya fara tashi ya haura sama sabida so yake yaje ya watsa ruwa.

Kafin nan sun watse a falon.

Ai kuwa tayarsa keda wuya.
Barrister Kabeer ya mi□e tare da cewa.
□□o mu zamu tafi Hafeez kaje maza kace Mamanka da Aunty Jannart su fito mu tafi □□.

Kai Ramadan da Riyyam-nsra suka □ago tare da zuba mishi idanu tare da cewa.
□□arrister da Aunty Jannart Kuma?□□.
Da sauri Baba Mau□o ya □aga musu hannu tare da cewa.
□□ayasa bakinku □□.
Yayi mgnar da alamun shima Abba da Barrister Kabeer sun sanar dashi yadda auren ya kasance.
Dr Sajo da Alhaji Bala Tambari kuwa kai suka jinjina tare da ha□a baki wurin cewa.
□□sky ni ban goyi bayan raba yarannan cikin wannan yanayin da suke cikiba □□.
Abban Rayyern ne ya □an jujjuya musu kai tare da cewa.
□□an Allah kada kuce komai □□.
Hakane yasa sukayi shiru.

Kana suka mi □e tare da yin sallama dasu suka tafi.

Dai-dai lokacin kuma Aunty Dijat da Jannart da Hafiza da Hafeez suka fito.
Wanda a tunaninsu Mamy Barrister Kabeer ya kiratane dan yayi mata nasiha shiyasa basu san me ake ciki ba.

Suna fitowa Barrister Kabeer yasa su Hafeez a gaba,
Abban Rayyern kuwa cikin tausasawa yace.
□□annart kije wurin Abbanki akwai mgnar da zakuyi, gobe da safe zanzo □□.
Cikin sanyi tace.
□□oh Abba □□. Kana tabi bayan Aunty Dijat, ta rasa wanne irin yanayi takeji.

Su kuwa su Baba Mau □o rakasu sukayi har waje.
A tare Dr Sajo da Alhaji Bala Tambari, da Barrister Kabeer suka fita gidan.

Suna fita Abba da Baba Mau □o kuwa, suka wuce □akin Baba Mau □o suka zauna.

Su Mamy kuwa jin shiru-shiru ne yasa suka, fito falo.
Ganin basa nanne yasa suka tambaya ina Jannart cikin sauri Riyyam-nsra yace.
□□humm su Abba sun sa, tabi Barrister Kabeer.□□
Cike da mamaki
Sukace.
□□eyasa □□. Kai suka jinjina musu alamun suma basu saniba.

Kai Mamy ta jinjina tare da zama a □asa gaban Mammy tace.
□□hummm tabbas akwai wata matsala dan tun jiya naga alamun hakan amman ni kaina bansan menene ba, amman in sha Allah zan bincika mana a daren nan □□.
Ita kuwa Mammy cikin sanyi tace.
□□oh ko dai □an naki yayi wani laifin ne □□.
Kai Mamy ta jinjina kana ta juyo ta kalli Ramadan tare da cewa.
□□aima ina zaton akwai matsala a lamarin aurenka nan da kyar in ba □aga bikin akayi ba □□.
Cikin wani irin zabura Ramadan ya zazzaro idanu waje tare da cewa.
□□nnalillahi wa innailaihi raji'un dan Allah Mamy kada ki sake fa □an haka wlh zan iya suma □□.
Cikin tsare fuska Mammy tace.
□□afi daga nan ba kunya □□.
Jin hakane yasa ma kawai ya haura sama, yayinda Riyyam-nsra yabo bayansa.
□akin Ramadan □in suka shiga, yana mai kiran Raihanansa.

A can side □in Baba Mau □o kuwa, cikin sanyi Abba yace.
□□aga yau zan dawo kwana nan Alhaji wanda akayi a bayama rashin sani ne □□.
Cikin dariya Baba Mau □o yace.
□□i tashi ka barmin □akina, kaje kaji da rigimar Ramadan in yaji an □aga auremsa.
Kafin gobe kuma muga iya tsaurin ido da rashin kunyar Rayyanu □□.

Kamar da wasa fa ma, amman ina fir.
Abba ya □i komawa cikin gida. Saida Baba Mau □o ya □ata fuska yayi da gaske kafin Abba ya mike ya nufi cikin gidan

Jannart kuwa suna shiga cikin mota, Aunty Dijat ta □an kalleta jin yadda hannunta □ aya ta □ata yayi zafi.
Cikin kula tace.
□□annart Zazza □i ko?□□.
Kai ta jujjuya mata alamun itama bata saniba.

A haka dai suka isa gida.

Suna shiga Su Hafeez suka kwanta bisa kujeru, shi kuwa Barrister Kabeer, zama yayi tare da cewa.
□□ijat ki shiga kitchen ki □an dafa mata ko indomie ne taci □□.

Jin haka yasa tana ajiye mayafinta ta shiga kitchen.
Ita kuwa Jannart kwanciya tayi bisa kujerar dake gefen Barrister Kabeer dan zazza □ in takeji sosai.

Shi kuwa cikin nitsuwa yaci gaba da tausar zuciyarta.

Rayyern kuwa cikin sanyi yake tako steps din yana mai sau □e ajiyan zuciya na kukan da yayi tayi,
Yayinda jikinsa kuma keta baza □amshi na musamman.
A hankali ya iso □an tsaya tsakiyar falon.
Kai ya □an sunkuyar ganin yadda Mamy da Mammy suka zuba mishi idanu.
Cikin sanyi yace.
□□ammy bakuyi bacciba □□.
Kai ta jinjina masa, Mamy kuwa cikin sanyi tace.
□□i yau kam kwanan zaune zamuyi, na yaushe gamo □□.
Kai ya □an jinjina kana cikin wasiyya ya nufi kitchen.
Fridge ya bu □e Chocolate nasa ya □an □iba, kana yana fitowa ya nufi falon Jannart □in.
Su kuwa da ido suka rakasa.

A can gidan Barrister Kabeer kuwa, da sauri Jannart ta tashi zaune lokacin da Aunty Dijat ta ajiye mata plate □in indomie da kwai a gabanta, tururin su ya bugeta.
A gigice ta nufi Bathroom dake cikin falon, tana maiyi wani irin masifeffen kakari da yun □urin amai,
Da sassarfa Aunty Dijat tabi bayanta.
Yayinda shi kuwa Barrister Kabeer cike da mamaki yake cewa.
□□ubahallahi lfy kuwa □□.
Ina babu mai bashi amsa, haka yasa ya rufa musu baya.

Tuni su Hafeez kuwa sunyi bacci.

Ita kuwa Jannart amai take cikin tsananin azaba, ga wani irin fitinennen zazzabin da takeji kamar zai kasheta.

Amai □in takeyi a gigice,
Wani irin duhune da jiri suka rufeta a tare,
haka yasa ta fita hayyacinta, sabida abubuwan sunyi mata yawa a wunin yauwa.

Da sauri Barrister Kabeer ya tallabeta tare da □agota cak, cikin ki □ima ya juya ya nufi waje yana cewa.
□□ubahanallahi Dijat zauna da yara bari in kaita adibiti □□.
Cikin tashin hankali Aunty Dijat tace.
□□a ilahi Abban Hafeez muje tare □□.
Yadda yaga har yanzu tana kakarin amai □in ne yasashi □ara gudu.
Bayan mota yasata, kana ya shiga gaba da yana labubo car key □in a aljihunsa.
Kafinma Aunty Dijat ta idosu har yaja motar.
Mai gadi kuma ya bu □e mishi gate yaja ya tafi.

Dole Aunty Dijat ta koma cikin gida.

Asibitin Dr Sajo ya wuce da ita, cikin Sa'a kuwa ya samu Dr Sajon dama asibitin ya nufa ba gidaba.
Amsarta akayi cikin gaggawa tare da bata taimakon gaggawan da suka samu aman nata ya tsaya,
Sannan aka farayi mata dukkan gwaje-gwaje da suka dace.

Da □an saurinsa ya fito falon yana cewa.
□□amy ina take ne?□□.
Cikin kauda kai Mamy tace.
□□aye □in?□□.
Da sauri yace.
□□annart mana, na duba bata falo a bedroom nasu Zaiton kawai na samu tana bacci har bathroom na duba bata nan, Mamy ina take?□□.
Da sauri duk suka juyo suka kalli □ofar falon jin muryar Abba na cewa.
□□a'adin ne ai ya cika, ba dama wata takwas ko shekara □aya kayi yarjejeniya da Barrister Kabeer cewa zaka sakar masa yarsaba, dan baka sonta ba kuma zaka ta□a sontaba dan haka yanzu sai ka rubuta takardar sakinta ka bani in kai mishi dan shi kam ya tafi da □arsa□□.

Kamar sau□ar aradu haka yaji kalaman Abba.
Lokacin □aya suka □unguza mishi lissafi da nitsuwa, cikin yanayin diriricewa yace.
□□i kuma?□□.

Ido Abba ya zuba mishi, tare da tsareshi dasu.
Cikin tsananin ki□ima yaji wata zufa ta keto masa, murya a sar□afe yace.
□□bba□□.
Da sauri Abba ya daka masa tsawar da tashi zamewa ya zauna □asa da □as, hannunsa duka biyu yasa ya dafe kansa.

Shi kuwa Abba gefen Mammy yaje ya zauna, a □asa kusa da matarsa, sunkuyar da kai yayi a matsayinsa na karami a kanta, cikin nitsuwa ya kora mata dukkan bayanan da Barrister Kabeer yayi masa.
Ita kanta Mamy jikinta yayi sanyi.
Mammy kuwa Kai kawai ta jinjina ta mi□a ta wuce □aki inda Zaiton take ba tare da tayi mgn ba.
Shima Abba mi□ewa yayi ya tafi.

Yana mai cewa Mamy ta biyoshi.
Haka ta mi□e ta bishi.
Ya zama sunyiwa Dr Rayyern watsiyar dila.

Wani irin tashin hankali yakeji mai gigitarwa.
Cikin fargaba ya mi□e da sauri ya haura sama.

Wayarsa ya □auka ya fara dannawa Barrister Kabeer Kira, sai dai wayar na shiga ba'a□agawa.
Sabida ya bar wayar a falon inda ya tashi.

A can asibiti kuwa cikin sau□e numfashi Dr Sajo ya kalli Barrister Kabeer dake zaune a gabansa cikin murmushi yace.
□□ongrat Barrister ka kusa samun jika nan da watanni takwas masu zuwa, dan Jannart nada cikene kimanin kwana ashirin da biyar zuwa wata □aya□□.
Cikin wani irin mamaki da tarin al'ajabi Barrister Kabeer ya mi□e tsaye.

A gidan Barrister Kabeer kuwa, da sauri Aunty Dijat ta amsa kiran Rayyern daketa shiga wayar Barrister.
Shi kuwa Rayyern yana jin an □aga yace.
□□hy! Why!! Whyyyyyyyyyy!? Barrister meyasa zakayi min haka □□.
Da sauri Aunty Dijat tace.
□□ayyern ba shi bane,.□□
Cikin sauri yace.
□□na yake □□.

□□a tafi Asibitin SAJOS HOSPITAL din Dr Sajo ya kai Jannart bata da lfy, sai amai takeyi kamar zata suma □□.
Cikin tsananin tashin hankali ya katse kiran.
Tare da zaran car key □insa.
 Gudu-gudu yake sau □owa har yana taka steps din bibbiyu.

Babu kowa a falon haka yasa ya fita.
Shiga motar yayi yana danna Ari horn a gigice hakane yasa ya wangale masa gate.

Kai tsaye SAJOS HOSPITAL □in ya wuce.
Yana isa yayi parking kana ya kusa kai cikin asibitin.
Kasan cewar lokacin sha biyu tayi, shiyasa babu zirga-zirgan mutane.

Kai tsaye ya wuce Office din Dr Sajo bisa jagorancin wata Nurse.
Suma isa wurin tace masa.
□□anne □□.
Kai ya jinjina mata kana ya kutsa kansa ciki.

Cike da tashin hankali ya kalli Barrister Kabeer dake □agowa daga sujjadar da yaji.

Yana ganinsa yace.
□□arrister ina matata?□□.
Cikin tsare fuska Barrister yace.
□□atarka adaba ai yanzu kam □iyatace, duk da kaci amanata ka karya al□awarin da kayi min ka rabata da budurcinta □□.
Cikin mamaki yace.
□□ allahi ni banyi mata komaiba ban rabata da budurcinta ba, amman ina son mamata dan Allah mu janye wanne sharadin amman wallahi tallahi billahil azeem ni ban kusancetaba ban keta budurcinta ba □□.
Cikin tsananin tashin hankali da tsoro Dr Sajo ya mi□a tsaye tare da cewa.
□□nnalillahi wa innailaihi raji'un Rayyern me kake fa□a haka kamar tatsuniya bayan Jannart har ciki take dashi na wata □aya sannan kake ratsewa kaga ga shaidar gwajin da mukayi mata □□.
Ya □are mgnar yana juyo masa takardar sikainin da sukayi mata.
Cikin wani irin yanayi mai wuyar ganewa ya fara jinjina kansa tare da cewa.
□□ allahi na rantse da girman zatin ubangijin ban kusancetaba ban rabata da budurcinta □□.
Cikin tsananin tashin, hankali, tsoro, ki□ima, gigita, Barrister Kabeer yace.
□□ai dan Allah ka dena raina min hankali da rantsewu to cikin na uban nawaye kenan?□□.
Cikin zubda hawaye ya fara jujjuya kai murya a raunace cikin gaskata wa yace.
□□a rantse da Allah da Manzonsa da kujerar al'arshi ban kusancetaba kuma cikin naw...!

Ba editing.

GARKUWAR taku ce dai MA'AURATA, da masu shirin aure, da masu jego, da yan gayu masu son k□□ mshi kece raini, da gyaran da zaike maimaita muku dararen forkon kuruciya

Ko kunsan Jikinmu na da sinadaran hormones da suke taimakawa dan □□ dam akan komai musamman lokacin da mace take mu □□ malar aure da mijinta. Mafi akasari wannan hormones din ne ke samun matsala ko su yi sanyi koma su daina aiki kwata-kwata shi ne dalilin da zai sa mace tace bata jin sha □□ wa ko bata san dadin aure ba. Albishirinku ina da kayan da ke taimakawa wannan sinadaran du dawo aiki tukuru don karkato miki da kimarki wajan mai gida sannan su taimakawa wannan sinadaran hormones dinki su dinka secreting din ni □□ ma wadatacciya da zata taimaka miki ki gamsu mijinki ya gamsu fiye da tunaninki. Note: Kayana ba sa tsinka ruwan ni □□ ma suna dai taimakawa hormones dinki ne su tsattsafo da ni □□ mar musamman wacca cutar sanyi ko dattin mahaifa ya dankarar da su ya hana su yin aikinsu yanda ya kamata. Haka zalika idan kina da kyau ki kara da wanka. Zaki iya amfani da magani na na gargajiya wanda zai gyara miki sex hormones din kullum ki kasance cikin humidify wato cikin damshi mai albarka kamar yanda ake son mace. Yana gyara miki mara.

Sai kamshi. Hajiyata daure ki fara amfani da turarena ki ji irin salon kamshin sa salo ne da zai daidaita ki da mijinki ya kankaro miki da kimarki a wajansa. Siyan na gari mayar da kudi gida.

Ga masu bu □ ata ga number' wayata wanda nake whatsApp dashi 09097853276 kimin mgn ta whatsApp in har kin tabbatar kin shirya saya mu dai-dai ta, kayana ba □ anana bane, shiyasa bana harkan karanta, muddin kinsan baki shirya sayaba Please kada kiyi min mgn ki bari sai kin shirya ku □ inki a hannu, ba ina nufin kayana bana talaka bane, no akwai □ ananan set na masu karamin karfi, banson aimin mgn a □ atamin lokacin aiyukana a shirme baki shiryaba. Shine karantan da bana so.
0005388578 Jaiz bank AISHA GARKUWA ALIYU. In kin shirya ga number ta ga kuma account number ta wanda in mun gama mgn zaki turo kudin ki, kana insa miki kaya a mota, duk □ asar da kike kayana zaije gareki, amman fa in kinada dalilin zuwan nasune □□□□ sayan na gari meda kudi gida.

GARKUWAR MA'AURATA

By
GARKUWAR MARUBUTA
1/2/22, 16:17 - Auntyn: □□ iki kuma nawane kuma halatta ce".
Cikin zafin Barrister ya kuma daka mishi tsawa a hargitse yace.
□□ ai tafi daga nan, ko a garin ga □ a-ga □ a ayi haka, yoh in ba mahaukaci ba wa zai ji wannan tatsuniyar taka ya yarda.
Kaida bakinka kace kayi min al □ awarin bazaka kusanceta ba, sannan kaje kayiwa yarinya ciki yanzu kazo kana wani cewa wai kai baka rabata da budurcinta ba, kuma ciki nakane □□.

Cikin ha□i□anin gsky Rayyern yace.
□□aba Barrister ni yarone koni mahaukacine da zanyi ta rantse maka a kan □arya.
Da Allah fa na rantse maka, wlh wlh wlh ban kusancetaba, ban rabata da budurcinta ba, kana ciki kuma nawane, domin ni nasan wacece Jannart nasan matata tana nan a cikekkiyar budurwa, kana amintacciya ce a gareni. Batun wani tsohon al□awarin kuma ai yarintace tasa nayishi a bayan ma□□
Toh fa mgna ta□au zafi.
Kowa ya kafe a kan gskyarsa.
Shi kuwa Dr Sajo komawa yayi ya zauna yana sau□e numfashi domin yafi yarda da Rayyern sai dai ya bashi dariya da kalmar wai yarintace to acikin watanni takwas □in kenan ya girma.
Shi kuwa Barrister cikin asalin takaici da ba□in ciki yace.
□□ayyern yarinta ko□□.

Da sauri ya gya□a masa kai alamar eh.
Shi kuwa Barrister cigaba yayi da ceea.
□□o yanzu ka girma kenan.
baka kyauta minba, tunda kasan shara□inmu meyasa dakaji ka girman zaka meda min yata bazawara da sai ka barni in aura mata □an uwanta Azeez nasan shi yana sonta□□.
A haukace Rayyern yace.
□□ai Barrister kace duk abinda kaga dama, ai koda na kusanceta matatace halaliyata sadaki na biya.
Kuma da aurena a kanta kake wani cewa zaka aura mata wani.
To mugani muga yadda za'ayi a aura mata wani
Magwaji ya gwoda ya mugani□□.
Cikin fesar da numfashi Barrister yace.
□□a manta shara□inmu ne da alkawarin daka□aukarmin□□.
A fusace yace.
□□hara□in banza shara□in wofi, ni babu ruwana da wani makareren shara□i Mata matatace ciki kuma nawane, kuma wlh duk abinda ya samu matata da cikina za'a ga bala'i mai kai da□afa da fiffige yaseen ina son matata□□.
Cikin sanyi Dr Sajo ya kamo hannun Rayyern dake wani rawa da karkarwa ya ajiyeshi bisa kujera.
Kana ya kamo hannun Barrister shina ya ajiyeshi.
Kallon kallo sukeyiwa juna.
Cikin nitsuwa Dr Sajo yace.
□□r Rayyern mesa kace ciki nakane? Bayan kuma ka rantse baka kusancetaba□□.
Cikin tarin fargabar □udurin daya gano Abbansa da Barrister Kabeer suke dashi yace.
□□r in shi ba likita bane bai san cewa a duniya babu wani abu daya kai sperm sauri ba, to ka gaya mishi yasan da haka.
Jannart dai matatace kana cikin shaidun □aurin aurenmu.
Na sani nayi masa al□awarin bazan rabata da budurcinta ba a wancan lokaci da nakega zan iya rayuwa babu mace.
To amman ai banyi mishi al□awarin bazanyi wasa da ita, inji □umin jikinta ba,
Wallahi ban kusancetaba tana nan da budurcinta ko daren shekaran jiya na tabbatar da haka.
So amman lokuta da dama muna kasancewa tare da ita a matsayin mata da miji.
□aki□aya gado□aya filo□aya, manne da juna.
A lukuta ma bambanta na samu nitsuwa a jikinta, wanda nakeda ilimin irin wannan kan iya samar da ciki.
Domin kai ka sani ciki saurin shiga ne dashi. Banyi kokonton cikintaba.
Na kuma yi imani cikin nawane halattacce, domin ha□i□a sperm na kan iya wucewa jikinta da gudurin kasheta bamgiji.

Kuma Alhamdulillah wannan ma ya isheka ishara Barrister, nasan nayi kuskuren furuci a baya, amman haka ba yana nufin ni Rayyern wai zan saki matata bane □□.
Murmushi mai cike da mamakin tsaurin idon Rayyern. Dr Sajo yayi tare da jinjina kai tabbas mgnar sa gsky ne a duniya sperp yana cikin abubuwan da sukeda masifar sauri.
Kana a duk sanda na miji ya kamo, yana kawowane da kwayayen haihuwa dubu, masu tsinin baki, yayinda na mace □aya ne.
Na macen zaiyi ta fafutuka har ya samu yayi karo da a bokin rayuwa su ha □u su li □ e, su zama ciki.
Tabbas wannan amintaccen bincikene da likitocin duniya suka yarda dashi.
Yana kuma faruwa a lokuta da dama, har a kan balagazzun □an mata masu bu □awa □azaman samarinsu □afa wai da nufin ai wasa kawai zasuyi baza'a shigaba.
Daga wannan wasan kuwa ubangiji keyin ikonsa, sai kaji ciki ya samu.
Hattara gareku yan mata, dama zaurawa wlh ciki yana samuwa a haka, kuji tsoron Allah

Cikin sanyi ya kalli Barrister Kabeer da yake murtu □e da fuska kana a hankali yace.
□□ arrister wlh kamar yadda ya gaya maka, ciki na shiga a wannan yanayi, muddin dai yayi inzali a kanta, har ta kai ga yana jin □uminta, kuma haka ba yana nufin ya ratsa budurcinta bane, ka yarda dani wlh tallahi haka na faruwa da iginin ubangiji □ □.
Wani dogon numfashi Barrister Kabeer ya sau □e da □arfi tare da lumshe idanunsa.

Shi kuwa Rayyern a hankali ya sassauta murya cikin nitsuwarsa data fara dawowa yace.
□□ an Allah Barrister ina Jannart take, ina bu □atar kusa dani □□.
Cikin ha □e fuska Barrister ya mi □e tsaye tare da cewa.
□□ arinyar da kace baka sonta ka tssneta bazaka kuma ta □a sontaba, ta yaya, zan bar marainiyar Allah a hannunka bayan nasan ba sonta kakeyi ba, ai wannan bazai ta □a yiwuwa ba □□.
Yana fa □in haka ya fice
Shi kuwa Rayyern hannu biyu yasa ya dafe kansa tare da cewa.
□□ nnalillahi wa innailaihi raji'un, dan Dr ka taimaka min, wlh Barrister zai azabtar damu, yasa Abba nama yana fushi dani, dan Allah ka taimaka min a matsayinka na waliyin aurenta gareni □□.
Cikin sau □e numfashi Dr Sajo yace.
□□ ayi □o □arin hakan tun kafin ka sani, to amman Barrister Kabeer da Abbanka sun □i su saurareni, amman yanzu kayi ha □uri ka koma gida, muga abinda gobe zatayi □ □.
Da sauri yace.
□□ r ya zanyi in koma gida bayan Jannart bata tare dani, kuma batada lfy, ta yaya zan samu nitsuwa □□.
Ya □are mgnar kamar zaiyi kuka.
Shi kuwa Dr Sajo cikin son kwantar masa da hankaki yace.
□□ ayyern kabi mgnata ka koma gida, kaje kaji da iyayenka, ni kuwa nayi maka al □ awarin zan ji da Barrister Kabeer, ko dan cikin nan da Allah ya samar dashi a tsakaninku □□.
Ina Rayyern fa ya kasa fahimtar Yaren.

Haka ya tasa Dr Sajo a gaba da magiya.
Karshe dai sukaje dakin da aka kwantar da Jannart amman sai suka samu Barrister Kabeer ya kulle □ofar ya kuma □i bu □e wa.

Ranan haka dai Rayyern ya kwana kamar zautacce.

Ramadan kuwa, tunda ya kira Raihana ta shaida masa, tabbas Abbanta ya □aga aurensu.
Kuka yayi ta mata tamkar □an yaye, ita kanta taji ciwon abin to amman yaya zatayi mahaifinta ne, dole itan ta aro jarumta tana bashi ha□uri.

Riyyam-nsra kuwa falo ya fito yayi ta sana'asa ta bau□ewa Kekkyawar tarbiyya da akayi masa.

Mammy kuwa, da Zaiton baccinsu sukayi cike da farincin ha□uwar ahlinsu.

Mamy kuwa tunda Abba ya gaya mata abinda ke faruwa na shara□in auren Rayyern da Jannart, cikin sanyi tace.
□□mman dai yanzu duk wanda yaga Rayyern yasan yana son matarsa kuma suna zaman lfy, na sani lallai yayi kuskure amman kada a tsananta masa□□.
Cikin tsuke fuska Abba yace.
□□a yake ba ke akayiwa cin fuskar bako□□.
Da sauri ta jujjuya kai, kana a hankali kuma tace.
□□annan kuma gsky ni kaina banji da□in □aga auren Ramadan da akayi ba, kuma ma wai meyasa aka □aga fisabililahi fa?□□.
Zamanshi ya gyara yana kallonta yace.
□□urkin nasa ya bani gamsassun hujjojinsa kan batun a □aga aure.
Domin ya lura da rawan kan Ramadan.
Yace tabbas kada muyi gamgancin yi musu auren nan a irin ya wannan lokaci da kwanaki goma kacal ne suka rage a □auki azumin watan Ramadan.
Yace iyaye da yawa suna wannan gangancin da sakaci a aurar da yara gab da Ramadan, suzo tun kafin su gama marmarin juna da sau□e jarabar kuruciyarsu a kama azumi.
Sanadin wannan sai azo ma'aurantan suyi ta kusantar juna a cikin darare da rana duk da sunsan azumine, sai bayan salla ayi ta aikawa malamai tambaya ana cewa sabon aurene sunyi ta karya azuminsu.
To da za'ace iyaye su lura da wannan in dai azumi yazo sauran wata □aya ko kwana arba'in to a ha□ura da auren a kaishi bayan salla domin kiyaye darajar watan.
Ya □ara da cewa, yaga kan Ramadan yana rawa, zai iya yin komai, yace ya gansa daren jiya har sha□aya da rabi yana gidan sa.
Na kuwa gamsu dan wallahi Ramadan jarabebben yarone, marar ha□uri kinga idanun nan sa irin na Rayyern na fahimci duk jarabbabun yarane masu □an karen fitina, mace bazata samu sau□i a wurinsu ba, kawai dai shi Rayyern ya iya takunsa ne.
Shi kuwa wancan □an jaririn Riyyam-nsra □in in dai ba dandatsen taure zamuyi mishiba, na fahimci tabbas zai iya aikata komai□□.
Ya kare mgnar yana kwanciya tare da cewa.
□□acci zanyi kin gamsu da hujjar mahaifin Raihana ko□□.
Kai ta gya□a masa tare da kwanciya gefensa, ganin har □arfe biyu da rabi na dare.

Ana fitowa sallan Adusa.
Rayyern ya nufi □akin da Dr Sajo ya nuna masa daren jiya cewa, nan aka kwantar da Jannart.
Sai dai yana zuwa ya samu, babu kowa a □akin koda yaje Office □in Dr Sajo nanma sai ya samu a rufe.
Daya tambaya sai akace masa ai daga masallaci gida ya wuce.

Jiki a sa□ule yaje ya shiga motarsa cikin sanyin jiki ya nufi gida.

A falo ya samesu gaba □ayansu tea suke sha kamar kullum amman yau harda Baba Mau □o kana dasu Mammy da Zaiton.
Amman banda Ramadan da yake dur □ushe gaban Abba fuskarsa a kumbure,
Jiki a sa □ule ya zauna gefen Mamy dake kallonsa cikin tausayawa duk ya rame a dare □aya.

□□amy Mammy ina kwana □.
Cikin kulawa Mamy ta amsa, yayinda Mammy kuwa ta amsa a da □ile, sai kuma ya kalli Abba da Baba Mau □o da ko inda yake basu kallaba, cikin sanyi ya gaidasu, a fakaice suka amsa masa,
Riyyam-nsra da Zaiton ne suka gaidasa.
Cikin sanyi ya amsa, kana ya juyo ya kalli Ramadan dake cewa.
□□an Allah kuyi karo □esu kada auren nan dan Allah Abba Baba Mau □o ku taimaka min kugafa dun an gama komai sai ana gobe □aurin aure kuma ace an □aga.□
Cikin tsuke fuska Baba Mau □o yace.
□□oh mu dai munyi iya yinmu, sarki mai gaggawa sai dai in kaine zakaje ka basu ha □urin □.
Da sauri ya kuma juyowa ya kalli Abba dake cewa.
□□i ka tashi a gabana kasan bana son yawan magiyar banza da wofi □.

Mi □ewa yayi tare da sakin kuka kamar yaro ya haura sama yana cewa.
□□a shiga ukuna □.
Abin nasama dariya ya basu.

Bayan sun gama shan tea □inne Baba Mau □o ya fita.
Abba kuma yayi ciki.
Mammy □aki ta koma.

Ganin hakane yasa Rayyarn longo □ar da kai, cikin sanyi yace.
□□amy kijifa wai rabani da Janna zasuyi, Mamy ki bawa Abba ha □uri dan Allah.
Kai ta jinjina masa tare da cewa.
□□ayi hakuri zomuje wurinsa.□
To yace kana yabi bayanta.

Shiru yayi gaban Abba ya kasa cewa komai.
Shi kuwa Abba kai ya kauda tare da cewa.
□□unda baka da abincewa, tashi ka tafi, ka shirya dai □arfe takwas dai-dai zamuje gidan Kakanku Malam Mainasara.□
Da sauri ya gyara zamanshi tare dayin kasa da kansa kana murya a sanyaye yace.
□□an Allah kayi ha □uri, wlh bata da lfy tana bu □atar kulawata □.
Da sauri ya dakatar dashi tare da cewa.
□□icemin daga nan □. Dole ya tashi ya fita.
Daga nan side □in Baba Mau □o ya nufa.

Ita kuwa Mamy cikin nuna tana fushi da mijin nata kan matakin da suka □auka kan Rayyern □in ta fito kitchen ta fara aiki.
Ganin haka Zaiton ta shigo ta fara tayata.

Shi kuwa Rayyern cikin sanyi ya zauna gaban Baba Mau □o daya tsaresa da ido, cikin sanyi yace.
□□ah kai mahaifina ka taimaka wa zuciyata datake fuskantar abubuwa biyu lokacin □aya, farin cikin bayyanarku da warwarewar ko wanne □ullin da kuma fargabar rabani da Jannart.

Dan Girman Allah Baba Mau □o kayiwa Abba mgn ku dawo min datata, ko dan cikin da ke tsakaninmu.□
Cike da mamaki da kuma tarin farin ciki Baba Mau □o yace.
□□iki?□. Yayi tambayar a da □ile da danne farin cikinsa, shi kuwa Rayyern da sauri ya gya□a masa kai.
Sai kuma yayi saurin □ago kansa tare da cewa.
□□□r tasu da kace bakaso, bazaka kuma ta □a sontaba, kayiwa ciki dan zalumci ka rabata da budurcinta, duk da yarjejeniyar da kukayi da □anin mahaifinta?".
Da sauri ya fara jujjuya kai tare da cewa.
□□aba Mau □o ni ina son matata □.
Cikin danne murmushin sa, yace.
□□ai kaje ka gayawa Barrister ai tunda dashi kuka shara □in bada niba, maza bani wuri ka shirya zamuje gidanmu □.

Cike da □una ya fita.

Acan wurin Barrister Kabeer kuwa, kasan cewar anyiwa Jannart duk abinda ya dace, kuma Alhamdulillah ta warware, haka yasa, ya □auketa suka koma gida.

Yayinda Aunty Dijat kuwa take bata kulawa ta musamman.
Suna zaune a falon ta ganshi ya foto da tarin tsoffin takardun da yake ta □oyewa, duk kwana biyu ya shiga silin ya dubasu kamar □arawo.
Cikin sanyi yace.
□□annart kiyi ha □uri tun jiya anje an kaiwa Daddynki sammaci tare da takardar bada umarnin tsaresa, shida su Alhaji Abdu Tababa da kuma Dr Lukman, da sauransu.
Kuma duk an kamasu, suna tsare, domin nafi son ranar monday ayi komai a gama.
Wa□annan sune tarin shiduna tsoffi da sabbin.
Sannan kuma a ranar za'a saki Junaid sabida zamansa a can yayi nitsuwa ta ha□i□a da tuba ma gsky.
Sannan Yah Azeez dinkima zai dawo a satin nan.
Kana Abdul da Mom sai randa Azeez ya dawo in yayi musu bayani zasu zo ki gansu.
Wa□anan kuma takardun kadarorin mahaifinki ne, domin na mahaifinsu Rayyern kam na bawa Alhaji Bala Tambari tun tuni ya kai mushi duk nima a lokacin ban san cewa Baba Mau □o bane □.

Cikin zubda hawaye ta ajiye cup □in tea □in da take sha, murya na rawa tace.
□□bba yanzu kashe Daddy na za'ayi □.
Shima hawayen yake tsiyayarwa kana a hankali ya kauda kai tare da cewa
□□ima Jannart wannan kukan shi nake tayi tsawon shekaru, bana son rasa □an uwana duk da mugune ina sonsa, amman kuma sonsa bazai sa in karesaba □.
Daga nan kuma sukayi ta kuka, da kyar Aunty Dijat ta iya lallashinsu.

